سمندری گنبد

# SUNDUKI DAGA TEKU

(Hausa)




Shehun Darika Jagoran Ahlussunnah
Mahassasin Kungiyar Dawatul Islami Masani Maulana Abu Bilal

**MUHAMMAD ILYAS**

**Attar Qadiri Razavi**


Fassarar Hausa
Daga Shashen Fassara
Na Dawat-ul-Islam

سَمُندری گُنبد

Samundarī Gumbad

# SUNDUKI DAGA TEKU

Wannan waazi ya gabatane daga bakin malaminmu Shaykh-e-Tarīqat Amīr-e-Aĥl-e-Sunnat, Shugaban Dawat-e-Islami ʻAllāmaĥ Maulānā Abu Bilal Muhammad Ilyas Attar Qadiri Razavi دَامَتْ بَرَكَاتُهُمُ الْعَالِيَه a harshen Urdu. **Translation Department** Bangaren masu faasara liitatafan musulunci suka fassarashi Zuwa yaren Hausa.Idan an samu wani kuskure a fassarar kokuma wajen Rubutun, A sanar da Rukunin masu fassara ta hanyar akwatun aika sako kokuma ta Email, tareda kudure niyyar samun tagomashi [LADA].

**Translation Department (Dawat-e-Islami)**

Aalami Madani Markaz, Faizan-e-Madinah, Mahallah Saudagran, Purani Sabzi Mandi, Bab-ul-Madinah, Karachi, Pakistan

**UAN:** ☎ +92-21-111-25-26-92 – Ext. 1262

**Email:** 🖃 translation@dawateislami.net

**Sunduki Daga Teku**

Fassarar Hausa na 'Samundarī Gumbad'

◆

DUKKAN HAKKIN MALLAKA TSARARRENE

Copyright © 2024 Maktaba-tul-Madinah

Ba'ayarda da sake buga wannan littafi ba ta ko wane irin hanya kokuma juyashi ta kowane hali,ta hanyar sadarwa na zamani ko daukarsa da murya ,ko wata daga cikin hanyoyi batare da rubutaccen izini ba daga Maktaba-tul-Madinah ba.

**Bugu na farko :** Jumādal Ukhrā, 1446 AH – (Aprilu, 2024)

**Kamfanin Dab'I :** Maktaba-tul-Madinah

**Adadi :**

**ISBN:**

## DAUKAR NAUYI

A tuntubemu cikin sauki domin daukar nauyin buga littatafan addini domin Isal-e-Sawab da niyyar ladan ya riski iyaye ko 'yan uwa da suka rigamu gidan gaskiya.

**Maktaba-tul-Madinah**

Aalami Madani Markaz, Faizan-e-Madinah Mahallah Saudagran,
Purani Sabzi Mandi, Bab-ul-Madinah, Karachi, Pakistan

**Email:** maktabaglobal@dawateislami.net – maktaba@dawateislami.net

**Phone:** +92-21-34921389-93 – 34126999

**Web:** www.dawateislami.net

اَلۡحَمۡدُ لِلّٰہِ رَبِّ الۡعٰلَمِیۡنَ وَ الصَّلٰوۃُ وَ السَّلَامُ عَلٰی خَاتَمِ النَّبِیّٖنَ

اَمَّا بَعۡدُ فَاَعُوۡذُ بِاللّٰہِ مِنَ الشَّیۡطٰنِ الرَّجِیۡمِ بِسۡمِ اللّٰہِ الرَّحۡمٰنِ الرَّحِیۡمِ

## Addu'ā domin fara karatun littafi

ka karanta wannan Du'ā kafin kafara Nazari da karatun littatafan musulunci ko darasin addini zaka tuna duk abinda ka karanta, اِنۡ شَآءَاللّٰہ عَزَّوَجَلَّ:

اَللّٰھُمَّ افۡتَحۡ عَلَيۡنَا حِكۡمَتَكَ وَانۡشُرۡ
عَلَيۡنَا رَحۡمَتَكَ يَا ذَاالۡجَلَالِ وَالۡاِكۡرَام

### Fassara

**Ya Allah عَزَّوَجَلَّ! Ka Budemin Kofar Hikima da Ilmi kuma ka Lullubemu da Rahmarka! Ya Madaukaki mai Karamci!**

*(Al-Mustaṭraf, vol. 1, pp. 40)*

**Note:** kar amanta dayin salati-'Alan-Nabī ﷺ sau daya kafin da kuma gama Du'ār.

# Transliteration Chart

| | | | | | |
|---|---|---|---|---|---|
| ء | A/a | ڑ | Ř/ř | ل | L/l |
| ا | A/a | ز | Z/z | م | M/m |
| ب | B/b | ژ | X/x | ن | N/n |
| پ | P/p | س | S/s | و | V/v, W/w |
| ت | T/t | ش | Sh/sh | | |
| ٹ | Ṫ/ṫ | ص | Ṣ/ṣ | ھ / ہ /ۃ | Ĥ/ĥ |
| ث | Š/š | ض | Ḍ/ḍ | ی | Y/y |
| ج | J/j | ط | Ṭ/ṭ | ے | Y/y |
| چ | Ch | ظ | Ẓ/ẓ | ◌َ | A/a |
| ح | Ḥ/ḥ | ع | ‘ | ◌ُ | U/u |
| خ | Kh/kh | غ | Gh/gh | ◌ِ | I/i |
| د | D/d | ف | F/f | و مدّہ | Ū/ū |
| ڈ | Ḋ/ḋ | ق | Q/q | ی مدّہ | Ī/ī |
| ذ | Ż/ż | ك | K/k | ا مدّہ | Ā/ā |
| ر | R/r | گ | G/g | | |

# *Abubuwan da littafin ya kunsa*


SUNDUKI DAGA TEKU* .......................................................................1
Wani daya karanta Ṣalāt'Alan-Nabī a fili an Gafartamasa.............1
Ciwo a dan Yatsa.........................................................................4
Sumbatar Kofar shiga Aljannah a Kowace Rana ..............................5
An 'Yanta Bayi guda Biyu Saboda daga Murya a gaban Mahaifiya6
Zaka dinga samu ladan Hajji karbabiya{ Mabrūr} ..........................7
Makoci a Gidan Aljanna ...............................................................8
Mai sabawa Iyaye na haduwa da Ukuba tun a nan Duniya ...........9
Kurumtace ukubar Mai Kin Amsawa Mahaifiya............................10
Mahaiafa su daina saurin tsinewa 'ya'yansu..................................10
Kadawo Gida Daga Kasar waje idan Mahaifanka suka kiraka......11
Jariri yayi Magana !.....................................................................12
Tafiyar mil Shida akan Dutsen Fa mai Tsananin zafi kuma Dauke da Mahaifiya a Kafada ..........................................................13
Idan da ace Mazane Suke Haihuwa ba Mata ba ...! ........................14
Matar Aure ta chanchanci a Tausaya mata ....................................15
Bayani akan Hukuncin Shayarwa..................................................16
Wajibine yiwa Iyaye Biyayya kuda kuwa basu da nagarta ............16
Uwa ta jurewa Kashi da fitsari na yara a lokacin kuruciya............18
Gawar Mutum mai kama da Jaki...................................................18
Allah عَزَّوَجَلَّ Baya karbar duk wata Bauta Alhali Mai ita Yana sabawa Iyaye ..........................................................................19





www.dawateislami.net

Ga masu Zagin Iyayensu ........................................................................21
`Wadanda Za'a Sakale a Reshe a Gidan Wuta ................................22
Wuta daga Sama kamar Ruwan Sama............................................22
Kabari Ya Ruguza Kashin Kirji .......................................................22
Mutane Uku Bazasu Shiga Ajannaba .............................................23
Idan Rashin Fahimta Ya Gifta {Ana Fada }a Tsakanin Mahaifi da
Mahaifiya Kai Dansu Mai Yakamata kayi?...................................23
Idan Iyaye Suka Bayar Da Umarnin Cire Gemu,Kada Ayi Musu
Biyayya..........................................................................................24
Menene Mutum Zaiyi Idan Mahaifansa Suka Rasu Alhali Suna
Fushi dashi? ..................................................................................25
Biyawa Mahaifa Bashinsu ..............................................................26
Yana Da Lada Kai Ziyara Kabarin Mahaifa A Duk Ranar Juma'a
.......................................................................................................27
Tashar Madani Channel{Gidan TV} Tana Kawo Sauyi A Gidaje27
Kafa Ta Karye Domin Addu'ar Mahaifiya ......................................29
Mu Nemi Afuwar Mahaifanmu Ta Hanyar Rike Kafafuwansu
Dan su Tausaya ..............................................................................30
15 Sunnoni Da Wasu Halaye Yayin Tafiya Da Kafa ......................31

◆ ◆ ◆



www.dawateislami.net

اَلْحَمْدُ لِلّٰهِ رَبِّ الْعٰلَمِيْنَ وَ الصَّلٰوةُ وَالسَّلَامُ عَلٰى خَاتَمِ النَّبِيّٖنَ

اَمَّا بَعْدُ فَاَعُوْذُ بِاللّٰهِ مِنَ الشَّيْطٰنِ الرَّجِيْمِ بِسْمِ اللّٰهِ الرَّحْمٰنِ الرَّحِيْمِ

# SUNDUKI DAGA TEKU*

Duk irin Kasalar da Shaidan zai samaka ka daure ka Karanta wannan Littafi Gaba dayansa Zai karamaka Tsoron Allah, اِنْ شَآءَ اللّٰه عَزَّوَجَلَّ.

## Wani daya karanta Ṣalāt'Alan-Nabī a fili an Gafartamasa

Wani Dattijo mai Tsoron Allah yayi mafarki da wani mutum bayan mutuwarsa ya tambayeshi yaya Allah yayi dakai ? 'مَا فَعَلَ اللّٰهُ بِكَ?' Sai yace, 'Allah عَزَّوَجَلَّ Ya gafartamin duk zunubaina .' Sai Dattijon nan mai tsoron Allah yace, 'Mai yasa haka ?' Sai mutumin nan ya amsa 'Nakasance ina koyon Hadisi a hannun Malaman Hadisi, Duk lokacin da sukai salati ga Manzon Allah صَلَّى اللّٰهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم. Nima sai Nayi irin Salatin a Fili Haka nan Duk Mutanen dake wajen sai suma suyi Salatin

* Amīr-e-Aĥl-e-Sunnat دَامَتْ بَرَكَاتُهُمُ الْعَالِيَه ya gabatar da wannan Wa'azine a wajen taron Ijtimā' na Sati-Sati ran Alkhamis bayan sallar magrib na Dawat-e-Islami – Kungiyace bata siyasaba ta zamo ''Ruwan dare Gama Duniya '' wajen koyar da Quran da Sunnaĥ –Ran on 18th Rajab-ul-Murajjab, 1431 AH (July 1, 2010). Masu daukar nauyin Bugawa da gyare-gyare. [Majlis Maktaba-tul-Madīnaĥ]

Annabi Saboda haka, Allah عَزَّوَجَلَّ Ya Gafartamana Gaba daya Saboda Albarakar Salatin *(Al-Qaul-ul-Badī', pp. 254)*

صَلُّوْا عَلَى الْحَبِيْب     صَلَّى اللّٰهُ عَلٰى مُحَمَّد

Allah عَزَّوَجَلَّ Yayiwa Sulaymān عَلٰى نَبِيِّنَا وَ عَلَيْهِ الصَّلٰوةُ وَالسَّلَام Wahayi ya Umarceshi da yaje Gabar Kogin Maliya Domin yin wata Ibada Annabi Sulaymān عَلٰى نَبِيِّنَا وَ عَلَيْهِ الصَّلٰوةُ وَالسَّلَام Ya tafi shi da Mutanensa, Batare daya lura da komai ba. Saboda haka sai ya Umarci wani Aljani cewa ya shiga cikin Teku yazo masa da Labari. Aljanin nan y Buga Nutso a Teku bayan Fitowarsa sai yace, Ban iya zuwa chan kasan Tekun ba kuma ban samo komai ba'Sai Annabi Sulayman عَلَيْهِ السَّلَام Ya umarchi wani Aljanin da yafi na farko karfi da karfin nutso a Teku, Shima haka yaje ya nutse iya iyawarsa Amma bai samo komai ba shima ,Sai Annabi Sulayman عَلَيْهِ السَّلَام Ya Umarchi Babban Hadiminsa Āṣif Bin Barkhiyā رَحْمَةُ اللّٰهِ عَلَيْه.

Jim Kadan sai, Āṣif Bin Barkhiyā رَحْمَةُ اللّٰهِ عَلَيْه Ya dawo da wani sunduki mai daukar Ido yana kyalli san nan yanada kususurwa hudu a kowacce kusurwa akwai kofa, ya Ajiye wannan Sunduki a gaban Annabi Sulaymān عَلٰى نَبِيِّنَا وَ عَلَيْهِ الصَّلٰوةُ وَالسَّلَام. Daya daga cikin koffofin anyitane da Tagulla mai sheki, kofa ta biyu kuwa an yitane da Zabarjadi Gogagge, kofa ta uku anyitane da Zinariya kofa ta hudu anyitane da Yakutu.Duk da an bude dukkan kofofin amma babu ko digon Ruwa acikin Sundukin nan, a ciki kuma wani kyakyawan mutum ne ya chaba ado yana Gabatar

da Sallah,Bayan ya idar da Sallar ne sai Annabi Sulaymān عَلٰی نَبِیِّنَا وَ عَلَیْهِ الصَّلٰوةُ وَالسَّلَام Yayimasa Sallama Yakuma Tambayeshi Labarin Wannan Sunduki. Cikin Girmamawa Yace Ya Manzon Allah (عَلَیْهِ السَّلَام)! Mahaifina yanada Nakasa Mahaifiyata kuma bata gani [i.e. Makauniya]. Nayi musu Hidima har ta shekaru, اَلْحَمْدُ لِلّٰه عَزَّوَجَلَّ. Mahaifiyata tayimin Addu'a kafin mutuwarta, 'Ya Allah (عَزَّوَجَلَّ)! Kabawa Dana Rayuwa mai Albarka ka sashi yazamo Mutumin kirki kuma ka gafartamasa.' Mahaifina shima yayi mini Addu'a lokacin mutuwarsa, 'Ya Ubangiji (عَزَّوَجَلَّ)! Kasa Dana ya Bautamaka irin wajen da Shaidan bazai dameshi ba.'

Bayan Mutuwar Mahaifana, Nazo bakin Bahar Maliya sai na shiga wannnan Sunduki. Daga nan kuma, Mala'ika ya dauki Wannan sunduki aka ajeshi a chan kasan Bahar Maliya. Annabi Sulaymān عَلٰی نَبِیِّنَا وَ عَلَیْهِ الصَّلٰوةُ وَالسَّلَام, Ya Tambayeshi shekarunsa Dan Saurayin nan Ya Fadasa, 'Nazo nan da irin Shekarun Annabi Ibrâĥīm Khalīlullâĥ عَلٰی نَبِیِّنَا وَ عَلَیْهِ الصَّلٰوةُ وَالسَّلَام.' Annabi Sulaymān عَلٰی نَبِیِّنَا وَ عَلَیْهِ الصَّلٰوةُ وَالسَّلَام Ya Fahimci cewa ya Rayu a Cikin Sundukin nan Shekara Dubu Biyu ya shafe a cikin Sundukin nan Amma kuma gashi har yanzu a Saurayi yake, Bashida Furfura ko Kwaya daya a kansa.

Bangaren Abinci kuma yace, Kowace Rana wata Koriyar Dabba che take kawomin wani kalar Abinci Rawaya a Bakinta, Duk sanda naci Abincin nan zan samu yana tattare da duk wani dadin Abinci na Duniyar nan. Yana samin koshin Abinci da



www.dawateislami.net

Ruwa duk a lokaci daya .Nakubuta kuma daga Zafi, Sanyi, Bacci, Kasala, Kadaici, Tsoro da Abin Tsoro. اَلْحَمْدُ لِلّٰه عَزَّوَجَلَّ'. Daga nan, Sai Saurayin nan ya nemi Izni daga Annabi Sulaymān عَلٰى نَبِيِّنَا وَ عَلَيْهِ الصَّلٰوةُ وَالسَّلَام, Āṣif Bin Barkhiyā رَحْمَةُ اللهِ عَلَيْه Ya dauki wannan Sunduki ya kaishi bakin Teku. Daga nan, Annabi Sulaymān عَلٰى نَبِيِّنَا وَ عَلَيْهِ الصَّلٰوةُ وَالسَّلَام Yace , 'Yaku Mutane ! Allah عَزَّوَجَلَّ Yayi mana Gafara Baki daya ! Ya Jama'a kun lura da Yadda Addu'ar Iyaye Take Saurin Karbuwa ! Mu Guji Sabawa Iyaye .' *(Rauḍ-ur-Riyāḥīn, shafi. 233)*

Allah عَزَّوَجَلَّ Yaji Kanmu ya yafemana Kura-kurenmu ya gafartamana Zunubanmu dan Darajar sa.

صَلُّوْا عَلَى الْحَبِيْب     صَلَّى اللّٰهُ عَلٰى مُحَمَّد

Yaku 'Yan Uwana a Musulunci! Yazama Dole akanmu yiwa Iyayenmu Biyayya, Jin dadin abin da mukayi musu zaisa su yi mana Addu'a ta cigabanmu a Duniya da Lahira:

## Ciwo a dan Yatsa

Sayyadi Abuyazīd Bisṭāmī قُدِّسَ سِرُّهُ السَّامِي yace, 'Wata Rana ana Tsananin sanyi, Sai Mahaifiyata ta Umarceni da Na Debo mata Ruwa. Nadebo Ruwan a Mazubi, Amma kafin na Karaso Wajen da take Har tafara Barci, Sai ni kuma naga Rashin Dacewar na tasheta daga barcin da take, Sai na Tsaya kusa da ita ina rike da Ruwan a Hannuna ina Jiran idan ta Farka sai

nabata Ruwan. An dauki lokaci chan a wajen sauya Tsayuwa sai Ruwan ya Zubarmin a DanYatsana Saboda sanyin da a take wannan Ruwa ya zama Kankara a kan Dan yatsana.

Chan sai Mahaifiyata ta Farka, na mika mata Ruwannan. Hannuna yana Like da Mazubin nan saboda kankara.Nayi Kokarin Banbare Hannuna daga jikin Mazubin nan sai Fatar hannuna ta yage sai jini ya rinka zuba ba Kakkautawa, Sai Mahaifiyata ta Tambayeni Meye haka ? Nikuma na Labarta mata abin da ya faru, Sai ta daga Hannunta sama tayimin Addu'a tace 'Ya Allah عَزَّوَجَلَّ! Na yarda da shi .Kaima ka yarda dashi kayi masa Afuwa

*(Nuzĥa-tul-Majālis, mujallad. 1, shafi. 261)*

Ya Allah عَزَّوَجَلَّ Kayi musu Rahma ,Sannan kajikan mu Kasa Kar ayimana Bincike Domin Darajarsu!

صَلُّوْا عَلَى الْحَبِيْب　　صَلَّى اللهُ عَلٰى مُحَمَّد

## Sumbatar Kofar shiga Aljannah a Kowace Rana

Duk Mutanen da sukayi sa'a Iyayensu nada rai su Rinka Sumbatar Hannuwansu da Kafafuwansu kowace Rana Da'akwai Lada mai yawa ga wanda yake kyautatawa Mahaifansa da kuma Girmamasu. Manzon Allah صَلَّى اللهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم Yace , 'اَلْجَنَّةُ تَحْتَ اَقْدَامِ الْاُمَّهَاتِ *Aljannah tana Duga-Dugan mahaifa*'

*(Musnad-ush-Shaĥāb, mujallad. 1, shafi. 102, Ḥadīš119)* Saboda haka, Kyautatawa Iyaye yana nufin Ajannah ce ga meso.

Yazo acikin *Baĥār-e-Sharī'at* – shafi 88, sashi na16 Ya kunshi shafi 312 – Dab'in Maktaba-tul-Madīnaĥ, Bangaren Dab'i na Dawat-e-Islami: Zaka iya sumbatar kafar Mahaifiyarka .Yazo a Hadisi 'Duk wanda ya sumabci kafar Mahaifiyarsa kamar ya sumbaci kofar Aljanna ne.' *(Durr-e-Mukhtār, mujallad. 9, shafi. 606)*

## An 'Yanta Bayi guda Biyu Saboda daga Murya a gaban Mahaifiya

Aduk Lokacin da kaga mahaifiyarka tana zuwa ko Mahaifinka , idan a Zaune kake ka mike tsaye saboda girmamawa .Kada kana Magana kana kallon cikin idanuwansu.ka sunkuyar da kanka idan suna Magana dakai , duk sanda suka kiraka ka amsa da 'Labbayk' (*Na'am* ). Kayi Magana dasu a cikin sanyin murya. Kada ka taba daga murya akan ta mahaifanka. Sayyidunā 'Abdullāĥ Bin 'Awn's Mahaifiyarsa ta taba kiransa a wajen amsawa sai ya dan daga Muryasa a kan ta mahaifiyarsa sai رَحْمَةُ اللّٰهِ عَلَيْه ya nemi Afuwa kuma ya 'yanta bayi biyu saboda yana ganin hakan zaisa ayi masa afuwa.

*(Ḥilya-tul-Awliyā, mujallad 3, shafi. 45, Ḥadīši 3103)*

صَلُّوْا عَلَى الْحَبِيْب     صَلَّى اللهُ عَلٰى مُحَمَّد



www.dawateislami.net

## Zaka dinga samu ladan Hajji karbabiya{ Mabrūr}

سُبۡحٰنَ اللّٰـه عَزَّوَجَلَّ! Tsarki ya tabbata ga Ubangiji ku lura da yadda Waliyyanmu رَحِمَهُمُ اللّٰهُ الْمُبِيْن suke, da yadda suke girmama Iyaye da kuma irin Yadda tunanisu yake ! Ina zamu samu bayi har guda biyu! toh! A irn wannan hali, Bamuda Karfin Zuciyar yin Sadaka da kaji guda biyu ma,Kai wasu ko kwai biyu bazasu iya bayarwa a hanyar Allah عَزَّوَجَلَّ ba. Allah عَزَّوَجَلَّ Yasa mugane Matsayin Iyayenmu Āmīn!

Yanzu bari na fadi Hanyar samun Lada Batare da kashe ko Sisi ba, kawai ka kalli fuskar mahaifanka da tausayawa da Soyayya da jinkai ,mai yafi dadi kamar kallon mahaifa da Tausayawa! Manzon Allah صَلَّى اللّٰهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم Yace , 'Idan Da ya kalli mahaifansa kallon jinkai da tausayawa , Allah عَزَّوَجَلَّ Zai rubuta masa ladan Mabrūr (Karbabben aikin hajji) ga dukkan kallo.' Sai Sahabbai رَضِىَ اللّٰهُ عَنۡهُم Suka tambaya , 'Koda mutum yayi irn wannan kallon sau dari ?' Masoyinmu kuma Annabin tsira صَلَّى اللّٰهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم yace, 'نَعَمْ، اَللّٰهُ اَكْبَرُ وَ اَطْيَبُ *yace Na'am, Allah* عَزَّوَجَلَّ *Madaukakine kuma Aṭyab (Mai tsarki).*'

*(Shu'ab-ul-Īmān, mujallad 6, shafi. 186, Ḥadīš 7856)*

Babu ko Shakka, Allah عَزَّوَجَلَّ Yana da ikon yin komai. عَزَّوَجَلَّ Zai iya raba irin wannan ladan ga wanda yaso, عَزَّوَجَلَّ Domin shi mabuwayi ne ba'abin dake gagararsa;Idan mutum yakalli mahaifansa da girmamawa ko sau dari ne shi kuma Allah عَزَّوَجَلَّ Zai bashi ladan Karbabbiyar hajji guda dari

صَلُّوْا عَلَى الْحَبِيْب صَلَّى اللّٰهُ عَلٰى مُحَمَّد

## Makoci a Gidan Aljanna

Wata Rana Annabi Mūsā عَلٰی نَبِیِّنَا وَ عَلَیْهِ الصَّلٰوةُ وَالسَّلَام Ya Tambayi Allah عَزَّوَجَلَّ, ‘Ya Mai Gafara ! Ka nunamin mutumin da zanyi makotantaka dashi a Aljanna ’ Sai Allah عَزَّوَجَلَّ Yace kaje gari kaza da kaza zaka sameshi achan kuma Mahaucine , Shine makocinka a Aljannah. sai Annabi Mūsā عَلٰی نَبِیِّنَا وَ عَلَیْهِ الصَّلٰوةُ وَالسَّلَام Ya tafi wannan garin domin haduwa da mahaucin ,Bayan yaje yanemishi sun hadu (Duk da yake mutumin nan bai sanshi ba sai a bako kawai ), Mahaucin nan ya gayyaci Annabi Mūsā عَلٰی نَبِیِّنَا وَ عَلَیْهِ الصَّلٰوةُ وَالسَّلَام. Gidansa,Lokacin da suka zauna dan cin Abinci sai ya Zauna a kusa da Wani Katon abu kamar Kwando. Bayan kawo Abinci idan yai Lauma ta abinci daya sai yasaka lauma biyu a cikin kwandon nan. Sai aka kwankwasa kofa, Mahaucin nan yatashi domin amsawa mai buga kofa .Annabi Mūsā عَلٰی نَبِیِّنَا وَ عَلَیْهِ الصَّلٰوةُ وَالسَّلَام kuma a gefe daya sai ya leka cikin Kwandon nan sai yaga Dattijai guda biyu Mace da Namiji . Ai suna hada Ido da Annabi Mūsā عَلٰی نَبِیِّنَا وَ عَلَیْهِ الصَّلٰوةُ وَالسَّلَام, sai Murmushi ya bayyana a fuskokinsu. Suka sheda da Annabcin Annabi Mūsā عَلٰی نَبِیِّنَا وَ عَلَیْهِ الصَّلٰوةُ وَالسَّلَام kuma a take suka rigamu gidan gaskiya .

Bayan Mahaucin na yadawo kuma ya tarar da Gawarwakin mahaifansa a cikin abun nan mai kamar kwando sai ya fahimci halin da’ake ciki. Sai yakama Hannun Annabi Mūsā عَلٰی نَبِیِّنَا وَ عَلَیْهِ الصَّلٰوةُ وَالسَّلَام yana sumbata yana cewa , ‘Lallai kai Annabin Allah ne, Mūsā Kalīmullāĥ (عَلٰی نَبِیِّنَا وَ عَلَیْهِ الصَّلٰوةُ وَالسَّلَام).’ Annabi Mūsā عَلٰی نَبِیِّنَا وَ عَلَیْهِ الصَّلٰوةُ وَالسَّلَام ya tambayeshi, ‘Yaya kayi



www.dawateislami.net

kaganeni ?' Ya amsa, ' Akullum mahaifana suna yin wannan addu'a kowace rana: Ya Allah (عَزَّوَجَلَّ)! Ka Albarkacemu da ganin Annabi Mūsā عَلٰی نَبِیِّنَا وَ عَلَیْہِ الصَّلٰوۃُ وَالسَّلَام a dai dai mutuwarmu, Nikuma saboda da yanda naga mutuwar tasu da sauri na gane an amsa musu burinsu kuma kaine Annabi Mūsā (عَلٰی نَبِیِّنَا وَعَلَیْہِ الصَّلٰوۃُ وَالسَّلَام).'

Mahaucin nan ya kara da cewa, 'Kuma aduk lokacin da Mahaifiyata taci Abinci taji dadi sai tayimin wannan addu'a : Ya Allah (عَزَّوَجَلَّ)! Kasa Dan nan nawa yazama Makocin Annabi Mūsā عَلٰی نَبِیِّنَا وَ عَلَیْہِ الصَّلٰوۃُ وَالسَّلَام a Aljanna.' Annabi Mūsā عَلٰی نَبِیِّنَا وَ عَلَیْہِ الصَّلٰوۃُ وَالسَّلَام Yace, 'Ina tayaka Murna ! Allah عَزَّوَجَلَّ Ya mayar dakai Makocina a Aljanna.' *(Nuzĥa-tul-Majālis, mujallad. 1, shafi. 266)*

Allah عَزَّوَجَلَّ Ya jikansu da Rahma ,Ya Gafartamana batare da Bincikeba, Domin Albarkar su!

## Mai sabawa Iyaye na haduwa da Ukuba tun a nan Duniya

Yaku 'yan uwana a Musulunci! Duk munji yadda Allah yake saurin amsa addu'ar iyaye ! haka kuma, Idan iyaye suka tsinewa 'ya'yansu a cikin fushi, Shima da irin tasirin dayake a tattare da 'ya'yan. Saboda haka koda yaushe mu rinka saka iyayen mu farin ciki, Babba dan Babba Cikamakin Annabawa صَلَّی اللّٰہُ عَلَیْہِ وَاٰلِہٖ وَسَلَّم Yace, 'Mahaifanka sune Wutarka da Aljannarka.' *(Sunan Ibn Mājaĥ, mujallad 4, shafi. 186, Ḥadīš 3662)*

A wata maganar tasa, Tsira da Aminci su Tabbata Agareshi صَلَّی اللّٰہُ عَلَیْہِ وَاٰلِہٖ وَسَلَّم Yace, 'Idan Allah عَزَّوَجَلَّ yaso yakan عَزَّوَجَلَّ Jinkirta

Ukubar duk wani sabo har sai a Alkiyama, Amma shi عَزَّوَجَلَّ Yana Ukuba gamai sabawa mahaifansa tun a nan Duniya.'

*(Al-Mustadrak, mujallad. 5, shafi. 216, Ḥadīš 7345)*

## Kurumtace ukubar Mai Kin Amsawa Mahaifiya

An Ruwaito cewa Mahaifiyar wani Mutum ta kirashi shikuma bai amsaba Mahaifiyar nan tasa ranta yabaci matuka sai ta Tsine masa a take kuma sai ya Kurumce saboda Addu'ar mahaifiyarsa. *(Bir-rul-Wālidayn liṭ-Ṭarṭūshī, shafi. 79)*

## Mahaiafa su daina saurin tsinewa 'ya'yansu

Yaku 'yan uwa musulmi! Kun lura ko! Wanda yaki Amsawa Mahaifiyarsa kira zai iya zama kurma a nan take ko! Wannan yazama ka'ida a kanmu da wa'azi bawai kawai ga yara marasa tarbiyaba a'a har ga Iyayenmu, zakaga mahaifiya tana cewa da danta: *Allah ya kasheka, ya hadaka da cutar Kuturta*, etc. Yakamata iyaye su yi taka tsan-tsan akan kalamansu akan 'ya'yansu kada a rashin sani su tsinewa 'ya'yan nasu a irin lokutan da ake amsa Addu'oi, Hakan zai zamo masifa ce ga 'ya'yannasu da su kansu iyayen da dukkan al'umma baki daya saboda yanda tsiniwar zatabi ta kan kowa saboda abin da'ya'yan zasu zamo a dalilin tsinuwar, Abu mafi dacewa shine yin addu'a a garesu da neman Allah ya shiryasu.

## Kadawo Gida Daga Kasar waje idan Mahaifanka suka kiraka

Babu kokwanto akwai daukaka kayi tafiya acikin Tawagar masoya Annabi ta Madanī Qāfilaĥs ta Dawat-e-Islami izuwa wurare da kasashe a fadin duniya kuma ka zauna achan wata 12 ko 25 Madanī Qāfilaĥs Domin kara Bunkasa Ayyukan Dawat-e-Islami.Duk da haka, Idan mahaifanka suka ji kewarka har hakan yasa basuji dadin hakan ba kokuma suka fada damuwa. Kokuma tun farko tafiyar taka zata basu rashin jindadi to wajibine karma katafi, ko idan suka nemi kadawo gida to kadawo gida. Yada aiyyukan Dawat-e-Islami Ga Dukkan Duniya hakika aikine domin neman yardar Allah عَزَّوَجَلَّ, Ba domin Yaban mutane ba .Ita kuma Yardar Allah عَزَّوَجَلَّ Bazata taba samuwa ba tare da Musgunawa Mahaifa ba .

Hakakuma dukkan tafiyar dazakayi ta Kasuwancice ko ta Aiki a Garinkune ko a Kasar waje kada kayi tafiyar har sai kasamu amincewar mahaifanka .Ka lura sosai da wannan ka'ida ,Yazo acikin shafi na 202 of *Baĥār-e-Sharīʿat*, sashi 16 [Amma 312 a Dab'in Maktaba-tul-Madīnaĥ, Bangaren Wallafa da Dab'I na Dawat-e-Islami]: I dan shi yana kasar waje , sai mahaifansa suka kirashi , [Anan] Dole ne sai ya koma. Rubuta wasika kadai bai wadatarba . Hakakuma , idan sun nemeshi yazo dan yai musu wani aiki tilas ne a kansa ya koma don bin umarnin iyayensa .

صَلُّوْا عَلَى الْحَبِيْب          صَلَّى اللهُ عَلٰى مُحَمَّد

## Jariri yayi Magana !

A duk lokacin da Mahaifanka suka kiraka lallaine ka amsa musu . مَعَاذَ اللّٰه عَزَّوَجَلَّ Wasu Mutanen basa damuwa sosai kuma basuma dauki kin amsawa mahaifa da wuri a matsayin koma ba Ka tuna ko kana Sallar Nafila ne suka kiraka Alhali basusan kana Sallah ba suna ta kiranka zaka sallame sallar ka tafi kiransu.' *(Baĥār-e-Sharī'at, mujallad 1,shafi. 638)* (Haka kuma wajibine ka sake wannan Sallar.]

Masu wulakanta Mahaifansu ta Hanyar kin Amsa Kiransu batare da daliliba sun Aikata babban sabo saboda haka sun chanchanci shiga Wuta . Uwa dai Uwace.Idan uwa ta tsinewa Danta koda da kuskurene a irin lokutan da ake amsa addu'a sai kaga Dan ya shiga matsala, Wannnan zai zamar mana izna ga abin da yafaru ga wani Babban Bawan Allah a Banu Isra'il, Wanda labarinsa yazo acikin littafin *Ṣaḥīḥ Bukhārī*: Manzon Raḥmaĥ, Mai ceton al- Ummaĥ صَلَّى اللهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم yace, 'Akwai wani mutum da'ake kira da Juraij a cikin Banu Isrāīla. Yana Gabatar da Ṣallāĥ, Sai Mahaifiyarsa ta kirashi Amma bai amsa ba. Yana tunani a ransa, 'Na amsa kiran mahaifiyata kokuma naci gaba da Sallah?' Mahaifiyarsa takuma kiransa sai ya zabi yaci gaba da Sallah daganan sai mahaifiyarsa ta (tayi masa Baki saboda yaki amsa kiranta), 'tace Ya Allah عَزَّوَجَلَّ! Kada kadau ransa har sai yaga fuskar Matar Banza.' {Karuwa}'

[Manzon Allah صَلَّى اللهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم Yaci gaba da cewa,] 'Wata rana, Juraij yana wajen dayake bautawa Allah عَزَّوَجَلَّ. Sai wata mata



www.dawateislami.net

tace , 'Sai na rinjayeshi' daga nan sai tafara zuwa tana neman Hira da Juraij amma baya amsa mata . Daga karshe sai taje wajen wani Makiyayi ta rinjayeshi ,Har suka haifi jariri kuma sai tace Dan nan nata na Bawan Allah Juraij ne . Mutane suka je wajen Juraij, Suka rushe Wajen dayake Bauta {ya gina Hasumiya achan yake shiga yana bautar Allah},Suka fito dashi suka Gaggaya masa maganganu marasa dadi. Juraij yayi Alwala yayi Ṣalāĥ yazo wajen Jariri nan yace masa , 'Kai! jariri waye Babanka! Yace Wanene Makiyayi , 'Da mutane suji sai sukace , Zamu gian maka wajen Bautarka {Hasumiya}da Zinare .'sai yace , 'A'a, ku mayar da ita kamar yadda take ta Kasa .' *(Ṣaḥīḥ Bukhārī, mujallad 2, shafi. 139, Ḥadīš 2482; Ṣaḥīḥ Muslim, shafi. 1380, Ḥadīš 2550)*

Ya Allah عَزَّوَجَلَّ Kajikan mu dan Darajarsa !

صَلُّوْا عَلَى الْحَبِيْب      صَلَّى اللّٰهُ عَلٰى مُحَمَّد

## Tafiyar mil Shida akan Dutsen Fa mai Tsananin zafi kuma Dauke da Mahaifiya a Kafada

Hakkin iyaye a kanmu nada yawa kuma ba'a daukemana ba. Wani Sahabi رَضِیَ اللّٰهُ عَنْهُ Wata rana yace da Manzon Allah صَلَّى اللّٰهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم, 'Akan Hanyar, Duwatsun da mukebi takansu sunyi zafinda da za'a saka danyen nama zai iya gasuwa ! Na dauki Mahaifiyata a kafadata har tafiyar mil shida. Shin Nagama



www.dawateislami.net

biyanta Hakkinta a kaina ?' Manzon Allah صَلَّى اللهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم Yace, 'Hakika, Wannan zai iya zama kashi daya daga cikin zafin Nakuda da wahala da tayi hakuri dashi yayin Haihuwarka.'

*(Al-Mu'jam-uṣ-Ṣaghīr liṭ-Ṭabarānī, mujallad. 1, shafi. 92, Ḥadīš 256)*

Allah عَزَّوَجَلَّ ya tausayawa Iyayenmu Ya Gafartamana ta dalilinsu!

## Idan da ace Mazane Suke Haihuwa ba Mata ba ...!

Ya 'yan uwa Musulmi ! Ba abin mamaki bane, Mahaifiya tana fuskantar wahalhalu a kan Danta , Mahaifiyace kawai tasan zafin Nakuda da wahalar dake tattare da haihuwa (i.e. Zafin da ta jure a wajen nakuda da haihuwar kanta). Maza Munci sa'a ba'a dora mana Nakuda da haihuwa ba .Babban malaminmu A'lā Ḥaḍrat, Imām-e-Aĥl-e-Sunnat, Mujaddidin Ummaĥ, Mai Farfado da Sunnaĥ, da Goge Bidi'a , Maulānā, Shāĥ Imām Aḥmad Razā Khān عَلَيْهِ رَحْمَةُ الرَّحْمٰن Ya fada acikin *Fatāwā Razawiyyaĥ*, Mujalladi 27, Shafi 101: Mace tana Fuskantar Wahalan a tsawon Lokaci, Abangare daya kuma Namiji shi jindadi kawai yasani. Mace kuwa na daukar ciki har na tsawon Wata Tara tana fama da wahalhalu ta wajen tafiya ,tashi daga zaune,da kuma zama da kwanciya, Sannan kuma ga Hadarin rasa rai gabadaya a duk nishin Nakuda. Sa'an nan kuma ga zubar jini na bayan haihuwa, har suna iya rasa Barcinsu domin haka. Shine yasa Allah عَزَّوَجَلَّ Yake cewa:

حَمَلَتْهُ اُمُّهٗ كُرْهًا وَّ وَضَعَتْهُ كُرْهًا ؕ وَ حَمْلُهٗ وَ فِصٰلُهٗ ثَلٰثُوْنَ شَهْرًا ؕ

*Mahaifiyarsa Ta Dauki Cikinsa A Wahalce Takuma Haifeshi A Wahalce Daukar Ciki da Yaye Shikuma Wata Talatinne.*

*[Kanz-ul-Īmān (Littafin Fassarar Quran)] (sashi 26, Sūraĥ Al-Aḥqāf, Aya ta 15)*

Saboda haka kamar ace an yanke mata Hukunci shekara uku da horo mai tsananine ga dukkan jaririn data Haifa. Idan da'ace Namiji zai iya haihuwar dan bera, da bazai kara yarda yakuma haihuwaba duk zawon rayuwarsa *(Fatāwā Razawiyyaĥ, mujallad. 27, shafi. 101)*

## Matar Aure ta chanchanci a Tausaya mata

Yaku 'yan uwa na musulmi! A Fatwā ta A'lā Ḥaḍrat رَحْمَةُ اللهِ عَلَيْه Yayi bayan yanda ya kamata a girmama Mahaifiya da kuma Mahimmancin Matar Aure, Miji ya kamata ya tausasawa matarsa musanman a lokacin da take da ciki, Ya rinka taimakon ta da Aiyukan Gida kuma kada yabarta tanayin aiyuka masu wahalarwa, kada kuma ya matsa mata kuma banda daga murya kai, dadai duk wata hanya dazata zama takurace a gareta, a takaice dai a barsu su huta kadda su wahala . Duka irin son da kakewa Danka, ya dace ka lura da uwar Dan naka da idanun tausayi da rahma [kuma ka tunawa kanka] Irin wahalar data sha kafin tabashi wannan dan nasa dayake matukar so.

## Bayani akan Hukuncin Shayarwa

A ayar Kur’anin da akayi bayani a baya acikin Fatawowin A’lā Ḥaḍrat رَحْمَةُ اللهِ عَلَيْه *‘Yaye wata Talatinne’*, yana nufin Alakar data faru a Dalilin shayarwa zuwa hani a Aure.

Yazo a shafi na 36 of *Baĥār-e-Sharī’at*, kasi na 2 [sahafi1182- A Dab’in Maktaba-tul-Madīnaĥ, Bangaren Bugawa da dab’I na Dawat-e-Islami]: Za’a Shayar da Jariri har shekara 2 a lissafin shekarar musulinci. Baya halatta shayar da jariri fiye da shekara biyu ga Namiji ne ko Mace.

Akwai wani Rashin fahimta a tsakanin mutane cewa wai idan jaririya Mace ce wai itace ake shayarwa shekara biyu I dan namijine kuma shekara biyu da rabi, wannan gabadaya ba daiadai bane , hukuncin nagaba dayane shine shekara biyu ba mace ba namiji .

## Wajibine yiwa Iyaye Biyayya kuda kuwa basu da nagarta

Sayyadi ‘Abdullāĥ Bin ‘Abbās رَضِىَ اللّٰهُ عَنْهُمَا Yace Manzon Allah صَلَّى اللهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم yace , ‘Duk mai biyayya ga Mahaifansa ,Kofofi guda biyu za’a bude masa dasafe Na gidan Aljanna, idan kuma mahaifan nasa dayane yarage da rai to za’a bude masa guda daya.Ga wanda kuma yake sabawa Allah عَزَّوَجَلَّ Ta wajen mahaifansa da yammaci , Za’a bude kofofi guda biyu na gidan wuta da safe , idan kuma mahaifan nasa saura daya hakan dai za’a bude masa kofa guda daya.’ Wani mutum ya tambaya, ‘Ko

mahaifan nasa suna cutar dashi.' Sai Manzon Allah صَلَّى اللّٰهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم ya amsa, Ko suna cutar dashi, Ko suna cutar dashi, Ko suna cutar dashi.' *(Shu'ab-ul-Īmān, mujallad. 6, shafi. 206, Ḥadīši 7916)*

Ya 'yan uwa musulmi! Duk mai kyautatawa mahaifansa yayi sa'a sosai. Kaga Mai kuntatawa mahaifansa yadau hanyar Tabewa a duniya da lahira. Allah عَزَّوَجَلَّ yace a Sūraĥ Banī Isrāīl, Aya 23 zuwa 25:

وَبِالْوَالِدَيْنِ اِحْسَانًا ؕ اِمَّا يَبْلُغَنَّ عِنْدَكَ الْكِبَرَ اَحَدُهُمَاۤ اَوْ كِلٰهُمَا فَلَا تَقُلْ لَّهُمَاۤ اُفٍّ وَّلَا تَنْهَرْهُمَا وَقُلْ لَّهُمَا قَوْلًا كَرِيْمًا ﴿۲۳﴾ وَاخْفِضْ لَهُمَا جَنَاحَ الذُّلِّ مِنَ الرَّحْمَةِ وَقُلْ رَّبِّ ارْحَمْهُمَا كَمَا رَبَّيٰنِيْ صَغِيْرًا ﴿۲۴﴾ رَبُّكُمْ اَعْلَمُ بِمَا فِيْ نُفُوْسِكُمْ ؕ

*Kuma ku kyautatawa iyaye, Koda yazamto Dayan sune ya Manyanta Tare da Kai kokuma Dukkansu, To kada ka Nuna Kosawarka dasu kada kuma ka Daka musu Tsawa kar kace dasu "Uff" kayi musu Magana ta Girmamawa. Kuma ka Kaskantar da Kai Garesu Don Tausayawa, Kakuma ce 'Ubangijina Kaji Kansu Kamar yadda suka Raineni ina Dan Karami. Ubangijine Mafi sani na Abinda Yake Zukatanku Idan kuka Zamo Nagari, To Hakika Lallai Shi mai Gafarane Ga Masu Komawa Gareshi da Tuba.*

*[Fassarar Quar'ani na [Kanz-ul-Īmān ] (Sashe Na 15, Banī Isrāīl, Aya 23-25)*

## Uwa ta jurewa Kashi da fitsari na yara a lokacin kuruciya

Ya 'yan uwana a musulumci! Cikin ayar da aka ambata a sama, Allah عَزَّوَجَلَّ Yayi umarnin kyautatawa iyaye kuma ya jaddada musanman a lokacin da suka tsufa. Tsufan mahaifa a gaskiya wata jarraba ce domin wani lokacin idan tsufaffine sosai suna iya yin kashi a gado ko ako ina kuma wajibine a kan 'ya'yan su gyara su .Ka tuna wajibine bin mahaifa koda kuwa a wannan hali.

A lura! Mahaifiyarka taci kashinka kuma taci futsarinka to yanzu kaima sai ka rama mata .Akwai iyayen da suke zama masu fada da zagi masu rigima saboda tsufa da cututtuka dole ne ka girmamasu kuma kai musu biyyaya , ayi musu wanka da wanki asa musu turare,kayi hakuri dasu iyakar iyawa karkace dasu '*uff*' balle har ka fada musu Magana marar dadi ,ka kiyaye idan kanaso kagama da duniya lafiya kuma kamutu kasadu da Allah kalau .

*Dil dukĥānā cĥor dayn mā<sup>n</sup> bāp kā*
*Warnaĥ is mayn ĥay khasāraĥ āp kā*

*Kadaina munanawa mahaifanka*
*Kokuma ka fada cikin Babbar Masifa*

*(Wasāil-e-Bakhshish, Shafi. 377)*

## Gawar Mutum mai kama da Jaki

Sayyidi 'Awwām Bin Ḥawshab عَلَيْهِ رَحْمَةُ اللّٰهِ الرَّب (Yana daya daga

cikin Tab'-e-Tābi'īn Ya rasu Hijira 148 ) Yace, 'Wata rana ian wucewa ta wata Unguwa kuma a karshen Unguwar akwai Makabarta . Bayan sallar La'asar, Kawai! Sai naga wani Kabari ya bude wani Mutum ya fito daga ciki amma mutumin yana da Kai kamar na Jaki kuma Ragowar jikin nasa irin na mutane ne sai yayi kuka {irin na jakai}sau uku sai ya koma cikin Kabari kuma ya Rufe da shi.

A gefe chan kuma akwai wata Tsohuwa tana aikin murza zare. Wata mata daga gefena kuma tace dani : Kaga waccen Tsohuwar? Sai na Tambayeta wacece,?' Tace, 'Wannan Tsohuwar daka gani itace Mahaifiyar wancen na cikin Kabarin. Mashayin Giyane. Duk lokacin daya sha yadawo gida da yamma, Sai Mahaifiyarsa tayi masa Nasiha ,Tace 'Yakai Dana ! Kaji Tsoron Allah عَزَّوَجَلَّ. Sai yaushene zaka daina shan Giya Marar tsarki !' Shikuma yakan bata amsa , Kina ta Ihu kamar Jaki.'Kullum haka sai Mutumin nan ya Mutu bayan Sallar La'asar. Tofa! Tun daya Mutu kullum sai Kabarinsa ya bude Bayan Sallar La'asar yafito yayi kukan Jaki sau uku sannan sai ya koma cikin Kabarinsa.' *(Attarghīb Wattarĥīb, mujallad 2, shafi. 226, Ḥadīš 17)*

## Allah عَزَّوَجَلَّ Baya karbar duk wata Bauta Alhali Mai ita Yana sabawa Iyaye

Yaku 'yan uwana a musulunci! Mu Tuba ga Allah عَزَّوَجَلَّ Cikakken mai Afuwa kuma mai Rahma.Mu Rokeshi Gafara domin dace a



www.dawateislami.net

Ranar Lahira. Ammafa! Kuntatawa Iyaye yana sakawa Mutum ya Wulakanta da Tartsatsin Azaba tun daga Kabrinsa har zuwa Ranar Alkiyama . Yazo Acikn Ḥadīši, ‘عَذَابُ الْقَبْرِ حَقٌّ’ *Azabar Kabari Gaskiyace* . *(Sunan Nasāī, shafi. 225, Ḥadīši 1305)*

Wasu Lokuta a kan Dan nunawa duniya saboda mutane su koyi darasi daga gareshi. A’lā Ḥaḍrat, Imām-e-Aĥl-e-Sunnat, Mujaddadin Al-Ummaĥ, Shāĥ Imām Aḥmad Razā Khān عَلَيْهِ رَحْمَةُ الرَّحْمٰن Yace a daidai lokacin dayake amsa fatawa akan wanda baya bin umarnin mahaifinsa: Kin bin Umarnin Mahaifi {Umarni ga abinda ba sabon Allah bane} Kin bin Umarnin Allah عَزَّوَجَلَّ Madaukaki ne Sabawa Mahaifi Sabawa Allah عَزَّوَجَلَّ. Idan Mutum ya Kyautatawa Mahaifansa, Sune Aljannarsa ,Haka kuma idan ya Saba musu Sune Wutarsa .Babu wani Aikinsa da za’a karba Na Farillane ko Nafila idan har baya Kyautatawa Mahaifinsa, kuma ana ji masa tsoron rashin yin kalamr Sahada a yayin Mutuwarsa ,Banda kuma azaba datake jiransa a Kiyama مَعَاذَاللّٰه عَزَّوَجَلَّ.

*(Fatāwā Razawiyyaĥ, mujallad. 24, shafi. 384-385)*

مَعَاذَاللّٰه عَزَّوَجَلَّ! Koda fa Iyayen Ba musulmi Bane,Yazama dole a kyautata musu ayi zumunci dasu Amma a iya dokokin da Shari’a ta ajiye. A Shafi na 452 of *Baĥār-e-Sharī’at*, mujallad [ 1182-shafi a Bugun da Maktaba-tul-Madīnaĥ, Bangaren Dab’I na Dawat-e-Islami], Ṣadr-ush-Sharī’aĥ, Badr-uṭ-Ṭarīqaĥ, ‘Allāmaĥ Maulānā Muftī Muhammad Amjad ‘Alī A’ẓamī عَلَيْهِ رَحْمَةُ اللّٰهِ الْقَوِى

Ya fada a cikin *'Ālamgīrī*, ' Idan Mahaifi ko Mahaifiya na musulmi kuma Mahaifan nasa ba Musulmi bane suka Umarce Dansu Musulmi daya kaisu {Temple} wajen Bautar Gunki da kar yabi Umarninsu anan Amma kuma idan Umarnin na Dawo dasu gidane daga wajen bautar Gunki zai iya zuwa ya dawo dasu Gida I *(Fatāwā 'Ālamgīrī, mujallad. 2, shafi. 350)*

## Ga masu Zagin Iyayensu

Mutanen da suke Zagin wasu da kalmomi marasa dadi Ba Mutanen Kirki bane ba . Masanin Shari'a , Hasken Darīqaĥ, 'Allāmaĥ Maulānā Muftī Muhammad Amjad 'Alī A'ẓamī عَلَيْهِ رَحْمَةُ اللّٰهِ الْقَوِى Ya fada a shafi 195 of *Baĥār-e-Sharī'at*, Kashi na 16 [Shafi na 312-Abugun Maktaba-tul-Madīnaĥ, Bangaren Dab'i na Dawat-e-Islami]: Manzon Allah صَلَّى اللّٰهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم Yace, 'Yana daga manyan Zunubai Mutum ya Aibata Iyayensa.' Sahabai suka Tamabaya, 'Yā Manzon Allah صَلَّى اللّٰهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم! Yaya mutun Zai Aibata iyayensa? sai صَلَّى اللّٰهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم yace , 'Kware kuwa ,Idan ka Aibata Mahaifin wani [kuma ] Shima dayan shima yarama da Aibata Mahaifin waccen; ko ya Aibata mahaifiyar mutum shima kuma yarama da Aibata mahaifiyarsa .' *(Ṣaḥīḥ Muslim, shafi. 60, Ḥadīši 146)*

A wannan hadisi, 'Malam Muftī Muhammad Amjad 'Alī A'ẓamī عَلَيْهِ رَحْمَةُ اللّٰهِ الْقَوِى yace, Sahabbai wadanda suka rayu a lokacin jahiliyya basu san cewa mutum zai iya Aibata Mahaifansa da suka haifeshi ba (i.e. Shine yasa suka ji

mamakin jin cewa mutum zai iya aibata mahaifansa). Manzon Allah صَلَّى اللهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم yayi musu bayanin me ake nufi da mutum ya Aibata mahaifansa. Amma a yanzu kuwa wasu ma dan rashin ladabi su da kansu suke Aibata Mahaifan nasu Saaboda rashin Ladabi garesu *(Baĥār-e-Sharī'at)*

## `Wadanda Za'a Sakale a Reshe a Gidan Wuta

Imām Aḥmad Bin Ḥajar Makkī Shāfi'ī عَلَيْهِ رَحْمَةُ اللّٰهِ الْقَوِى Ya ruwaito daga : Manzon Raḥmaĥ صَلَّى اللهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم yace, 'A daren Isra'i da Mi'irāji, Naga wasu Mutane a Sakale a sama suna reto a Reshin Gidan Wuta. Sai na tambaya, ''Yaa Jibrīl, Su waye Wadannan?' Ya amsa Yace, 'اَلَّذِيْنَ يَشْتُمُوْنَ اٰبَاءَهُمْ وَاُمَّهَاتِهِمْ فِى الدُّنْيَا *Wadannan sune mutanen da suke Aibata Mahaifansu Maza da Mahaifansu Mata a Duniya.*' *(Az-Zawājir 'Aniqtirāf-il-Kabāir, mujallad. 2, shafi. 139)*

## Wuta daga Sama kamar Ruwan Sama

An ruwaito cewa duk mai Aibata Mahaifansa ,Wuta na saukowa daga sama kamar Zubar Ruwan Sama a Kabarinsu.' *(Az-Zawājir 'Aniqtirāf-il-Kabāir, mujallad. 2, shafi. 140)*

## Kabari Ya Ruguza Kashin Kirji

An Ruwaito cewa, 'A lokacin da wanda baya Ganin Girman mahaifansa Yashiga Kabari Bayan an Binne shi, Kabari zai

Matseshi Matukar Matsewa Har Sai Kasusuwan Kirjinsa sun Karairaye na Dama sun Hade dana Hagu.

*(Az-Zawājir 'Aniqtirāf-il-Kabāir, mujallad,5 shafi. 140)*

## Mutane Uku Bazasu Shiga Ajannaba

Sahabi 'Abdullāĥ Bin 'Umar رَضِیَ اللّٰہُ عَنۡہُمَا Ya Ruwaito Daga Manzon Allah صَلَّى اللهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم Yace, 'Mutane Uku Bazasu Shiga Aljannah ba : (1) Wanda Iyayensa Ke Fushi Dashi. (2) Da Dayyūš {Wanda baya Kishin Matarsa Ta Aure} (3) Da Mace Mai Shigar Maza.' *(Al-Mustadrak, mujallad, 4 shafi. 252, Ḥadīš 252)*

## Idan Rashin Fahimta Ya Gifta {Ana Fada} a Tsakanin Mahaifi da Mahaifiya Kai Dansu Mai Yakamata kayi?

A'lā Ḥaḍrat, Imam-e-Aĥl-e-Sunnat, Maulānā Shāĥ Imām Aḥmad Razā Khān عَلَیۡہِ رَحۡمَۃُ الرَّحۡمٰن Yace: Idan Rigima ta Kaure a Tsakanin Mahaifa 'ya'yan su Bazasu goyi bayan kowa ba, ko Mahaifi Ko Mahaifiya , Kar su Wulakanta Babansu Dan Goyan Baya da Soyayyar Babarsu haka kuma kar su Koma bayan Babansu su Wulakanta Mahaifiyarsu, Ḥarāmunne kuma Sabawa Allah عَزَّوَجَلَّ. Ne kakoma kana zargin mahaifinka akan mahaifiyarka har ka kasa bashi hakkinsa akanka na Uba.Kar amanta mahaifanmu guda biyu Aljannarmuce Hakanan Kuma Wutar muce. Idan ka Mugustawa Mahifinka Wuta ce, وَالۡعِیَاذُ بِاللّٰہ (Allah عَزَّوَجَلَّ Muna neman tsari}. A kiyaye Ba'a Bin Abin Halitta Wajen Sabawa Mahalicci Allah عَزَّوَجَلَّ.

A Misali, Idan Maahaifiya ta Umarci Danta da Yin Rashin Ladabi Ga Mahaifinsa Don Farincikinta Sai Dan Yaki Aikatawa wato Yaki yin Rashin Ladabi ga Babbansa Sai kuma mahaifiyar tasa Take Fushi da Shi , Anan Bazai kula da Fushin taba. Hakama idan Mahaifin sane Yayi Umarnin ya Mugustawa Mahaifiyar tasa a nan ma Bazai yi abinda Mahaifinsa ya Umarce shiba.

Malamai Sun nuna cewa Mahaifiya tafi zama Mafi Mahimmanci a Wajen Yiwa Hidima akan Mahaifi , Malamai sun tafi akan cewa Shikuma Mahaifi Shine a kan Gaba Awajen Girmama wa, Domin shi Mahaifi Da Dan da Uwar duk suna Karkashin sane Dukkanninsu Ababen Ikonsa ne.

*(Derived from: Fatāwā Razawiyyaĥ, mujallad. 24, Shafi. 390)*

## Idan Iyaye Suka Bayar Da Umarnin Cire Gemu,Kada Ayi Musu Biyayya.

Ya Tabbata cewa Bazamu yiwa Iyaye Biyyaba idan abin da suka Umarcemu ya Sabawa Shari'a, Zai zama Sabo muyi musu Da'a. Misali idan Mahaifanmu suka Umarcemu da yin Karya kokuma Umarnin Aske Gemu kasa da kamu daya, Anan Baza aimusu Da'a ba duk irin Fushin da Zasuyi a irin Wannan Hali yi musu Biyayya shine Sabaawa Ubangiji Allah عَزَّوَجَلَّ.

Haka kuma idan aka samu Sakin Aure kuma Mahaifiya tayi Kokarin Hana 'Ya'yanta Zuwa Wajen Mahaifinsu. Ananma Za'a



www.dawateislami.net

Sabawa Umarnin Mahaifiyane Koda Kuwa Zatayi Kuka, Bawai Ziyartar Mahaifi Kawaiba a'a harda yimasa hidima,. Mutuwar Aure bata raba 'ya'ya da iyayensu Wannan Alakar tana nan Bata yankeba Hakama Hakkukuwa suma suna nan ana Bukatar a cika su.

## Menene Mutum Zaiyi Idan Mahaifansa Suka Rasu Alhali Suna Fushi dashi?

Wanda Duk Mahaifansa Suka Mutu Alhalin suna Fushi da shi, Babban abin dai Zaiyi shine yi musu Addu'a Ba dare ba rana , Domin ita Addu'a itace Babban Abinda zai riski Iyaye na Abinda Dansu Ya aikata . Sannan kuma dayin Aikin Alheri da Sunansu Da Nufin Allah yakai musu ladan Shine yin Īṣāl-e-Šawāb ga Mamatanmu Domin su sami Ladan aikin da Muka aikata Domin su , Yin haka akai-akai Mahaifanmu suna samun ladan Aiyukan mu Zaisa su Yafe mana Laifinmu a Wajensu.

An Anbata a shafi na 197 of *Baĥār-e-Sharī'at*, kashi 16 [Shafi na 312 a Dab'in Maktaba-tul-Madīnaĥ, A Bangaren Dab'I na Dawat-e-Islami]:Manzon Allah صَلَّى اللهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم Yace , 'Mahaifan Mutum ko Daya daga cikinsu ya Rasu kuma yakasance yana yi musu Rashin Da'a , To! Yayi ta rokarmusu Gafara a Wajen Allah عَزَّوَجَلَّ Har sai Ubangiji Ya Rubuta Sunansa a Cikin Bayinsa Nagargaru.' *(Shu'ab-ul-Īmān, mujallad. 6, shafi. 202, Ḥadīši 7902)*

Zaka iya Fansar Kananan Littatafai Da Manya daga Maktaba-tul-Madīnaĥ Kuma ka Rarrabasu a Kyauta Domin Mahaifanka dan Allah yasadasu da Ladan Īṣāl-e-Šawāb[1]. Haka kuma idan kanaso ' A Rubuta maka Suna Da Adireshi Ajikin Littafin daka Fansa Domin Īṣāl-e-Šawāb, A Tuntubi Maktaba-tul-Madīnaĥ.

## Biyawa Mahaifa Bashinsu

Manzon Allah صَلَّى اللّٰه عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم Yace, 'Dukkan Wanda Ya Biyawa Iyayensa Bakancensu (Bayan mutuwarsu) Kuma yabiya musu Bashinsu ; Kuma Bai Janyo Musu Zagi ba Ta Hanyar Zagin Iyayen Wasu , Za'a Rubuta sunanshi a cikin Masu Biyayya ga Mahaifansa, Koda kuwa a Yayinda Mahaifan nasa ke da Rai Baya Biyayya agaresu. Haka kuma Duk wanda bai Cikawa Mahaifansa Bakancensu ba kuma Bai Biya musu Bashisshi kansu ba kuma Yana Janyo Musu Zagi Ta Hanyar Zagin Iyayen Wasu Mai Wannan Hali Za'a Rubutashi A Wanda Baya Biyayya Ga Mahaifansa koda kuwa da suna da Rai Yakasance Yana Biyayya agaresu .' *(Al-Mu'jam-ul-Awsaṭ, mujallad. 4, shafi. 232, Ḥadīši 5819)*

صَلُّوْا عَلَى الْحَبِيْب　　صَلَّى اللّٰهُ عَلٰى مُحَمَّد

[1] Īṣāl-e-Šawāb Yana nufin Aikata wani Aikin Lada da Niyyar Riskar da Ladan ga Iyaye kokuma 'yanuwa.

## Yana Da Lada Kai Ziyara Kabarin Mahaifa A Duk Ranar Juma'a

Manzon Allah صَلَّى اللهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم Yace, 'Dukkan Wanda Ya Kai Ziyara Kabarin Mahaifansa Ko Daya Daga Cikinsu a Dukkan Ranar Juma'a Ubangiji Allah عَزَّوَجَلَّ Zai Gafarta Masa Zunubansa Kuma Za'a Rubuta Sunansa Acikin Masu Kyautatawa Mahaifansa.'

*(Jāmi' Tirmiżī, shafi. 97, Ḥadīši 130)*

## Tashar Madani Channel{Gidan TV} Tana Kawo Sauyi A Gidaje

Yaku 'Yan uwana Musulmi ! Domin kaucewa Sabawa Iyaye , Dakuma Kudure Niyyar Kyautata masu Dakuma Kokarin Yin Koyi Da Nuna Kaunar Ma'aikin Allah صَلَّى اللهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم A Cikin Zuciyarka ; Koda Yaushe Yakasance Kana da Alaka da Ma'abota Sunnah ta Dawat-e-Islami. اِنْ شَآءَاللّٰه عَزَّوَجَلَّ, Yin Haka Zaiyimaka Amfani Matuka Domin yin koyi Sunnaĥ, Da kuma Kyamar Aikata Sabo.

Domin Koyon Sunnah, Kayi Tafiya a Tawagar Madanī Qāfilaĥ ta Kwana 3 Kowane Wata Tareda Masoya Ma'aikin Allah عَزَّوَجَلَّ. Ka Tafiyar da Safiyarka da Yammacin a Ka'idar Cikin 'Madanī In'āmāt'[1] Wanda Madanī Markaz[2] Suka samar. Hakakuma, a duk dare yakamata kayi Fikr-e-Madīnaĥ[3] Akalla kayi Mintuna 12 Wajen Cike Madanī In'āmāt اِنْ شَآءَاللّٰه عَزَّوَجَلَّ, Zaka ci Riba Babba a Wannan Rayuwa ta Duniya Da Lahira. Saurara



www.dawateislami.net

Kaji Wani Tagomashi Da Albarka Da'ake Samu a Sauraron Dawat-e-Islami :

Wannan Shine Takaitaccen abinda ya Faru Kamar Yadda Wani Malami Mai Koyarwa a Dawat-e-Islami Daga Garin Mirpur 11 (Dhaka, Bangladesh): Yana kan Hanya Yana Tafiya Sai,Yahadu da Wani Mutum yana Tafe Shi da Matarsa da 'Ya'yansa, Sai Yace dani {Saboda Ganin Yadda Nasaka Suturata }, 'Shin Kasan Ina Zanje Nida Matata da 'ya'yana? Sai Yaci Gaba da Amsawa Kansa Tambayar da yaimin 'A Gaskiya Nasamu Matsala Nida Mahaifana Amma Yanzun nan Naga Wani Karatu {Wa'azi}a Madani Channel {Tashar TV ce ta Da'awat-eIslami } Mai Suna '*Mā$^n$ Bāp kay Ḥuqūq* (Hakkin Iyaye)' Anan na Gane Cewa Ashe ba Karamin Sabo nakeba Wajen Daina Yi Musu Biyayyah, Saboda Haka Yanzu daka Ganni Zanje Har Gida na Nemi Gafafarsu Nida Iyalaina Gaba daya. Allah عَزَّوَجَلَّ Yabawa Dawat-e-Islami da kuma Madani Channel Lada akan Abinda Sukeyi na Alheri.'

اٰمِيْن بِجَاهِ النَّبِيِّ الْاَمِيْن صَلَّى اللهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم

*Rāĥ-e-Sunnat per chalā ker sab ko Jannat kī ṭaraf*
*Lay chalay bas aik yeĥī ĥay Madani Channel kā ĥadaf*
*Yā Khudā ĥay iltijā 'Aṭṭār kī*
*Sunnatayn apnāyain sab Sarkār kī*

صَلُّوْا عَلَى الْحَبِيْب صَلَّى اللهُ عَلٰى مُحَمَّد

## Kafa Ta Karye Domin Addu'ar Mahaifiya

Yaku 'Yanuwa Musulmi! A Abinda ya faru a hikayar nan Ta Sama Da Wa'azantuwar da Jama'a Suke sama a Dalilin Madani Channel. Kamar Dai Wannan Wa'azi Na Bin Iyaye . Kaga Zaiyi Wuya Mu Tsira Daga Hakkin Iyayenmu Akanmu Duk Tsawon Rayuwarmu Kuma haka Kyautata Musu Shima Yana Kanmu Har Abada in Muna son Gamawa da duniya Lafiya. Babban Malami Kamāluddīn Damīrī عَلَيْهِ رَحْمَةُ اللّٰهِ الْقَوِى Ya Ruwaitar :Cewa Mal, Zamakhsharī (Babban Malamine kuma Ba Mu'utazilene shi) Kafar sa Daya a Gutsure take Amma da Mutane Suka Tambayeshi Akan Gutsurarriyar Kafarsa Sai Yace Hakan Ya farune Sakamakon Addu'ar Mahaifiyata .

Ya hau Bayani, Yace : Abin Ya Farune Tun Ina da Kuruciya,Wata Rana Nayi Tarko sai Nakama 'Yar Benu {Tsuntsuwace 'yar Karama} Sai Na Daura Mata Zare a Kafa . Chan Sai ta Kufce Ta Tashi Sama ta shiga Tsakanin Bangon daya tsage Ammafa Tata shi da Zaren nan kafarta . Nikuma Sai Na Kama Zaren nan Na Fizgo Tsuntsuwannan da Karfin Tsiya, Sakamakon haka Kafar Tsuntsuwar nan Ta Karye Ta kuma fita daga Jikinta Sai Tafito Tana Wani Irin Kuka, Ashe Duk Abinda Yake Faruwa Mahaifiyata tana Kallon Komai kuma Ranta Yayi Matukar Baci sai Tayi Min Muguwar Addu'a Tace' 'Allah kaima Ya Karya kafarka Kamar Yadda ka Karyawa Wannan Karamar Halitta Marar Karfi.' Bayan Wani Lokaci Kamar An Mance. Wata Rana, Ina Kan Hanyar Zuwa Garin 'Bukhara' Domin Neman Ilmin Addini. Muna Kan Hanya, Sai

na Fado daga Kan Abin Hawa na Naji Ciwo Sosai a kafata, Bayan Mun Sauka a Garin Bukhara, Nayi ta Magani Kala-Kala Amma Babu Sauki Sam Ta Dole sai da aka Yankemin Kafa Nasamu Sauki. (Ta haka, Addu'ar da Mahaifiyata Tayimin Allah عَزَّوَجَلَّ Ya Amsa mata).

*(Ḥayāt-ul-Ḥaywān-ul-Kubrā, mujallad. 2, shafi. 163)*

## Mu Nemi Afuwar Mahaifanmu Ta Hanyar Rike Kafafuwansu Dan su Tausaya

Yaku 'Yanuwa na Musulmi! Idan Mahaifanka Ko Daya daga cikinsu Yana fushi da kai, Batare da Bata Lokaci ba Ka nemi Afuwa daga Garesu kayi Kuka a Gabansu ka Hade tafikan Hannayenka ka Durkusa Kasa ko Zasuji Tausayinka Su Yafe Maka. Karka Manta Sune Cigabanka na Duniya Da Asararka A Duniya. Domin samun VCD Akan Hakkin Iyaye Yakamata ka samu Guda 2 Wanda Maktaba-tul-Madīnaĥ Suka buga :

1. Mā Bāp kay Ḥuqūq { Hakkin Uwa da Uba }
2. 'Wālidayn kay Nā-Farmāno kā Anjām'. Wannan VCD Ya kunshi karatun Madanī Mużākaraĥ Wanda akayi a I'tikāf a Watan Azumi (1430 Ĥijrī).

*Dil dukĥānā cĥor dayn mā$^n$ bāp kā*
*Warnaĥ ĥay is mayn khasāraĥ āp kā*

*Kīnaĥ-e-Muslim say sīnaĥ pāk ker*

*Ittibā'-e-Sahib-e-Lawlāk ker*

*Yā Khudā ĥay iltijā 'Aṭṭār kī*

*Sunnatayn apnāyain sab Sarkār kī*

*Mudaina Karya Zuciyoyin Mahaifanmu*
*Idan kuma munki Zamu Fada dukkan Masifa*
*Mu wanke zuciyoyinmu Akan yin Gaba ga musulmi*
*Kuzo Mubi Manzon Allah sau da kafa*
*Ya Allah, Wannan Shine Rokon 'Aṭṭār*
*Cewa Kowa da Kowa Ya Dawo Yabi Sunnar Maaiki*

صَلُّوْا عَلَى الْحَبِيْب صَلَّى اللّٰهُ عَلٰى مُحَمَّد

Yaku 'Yanuwana Musulmi! Wannnan Wa'azi Namu Yazo Karshe, Amma ina so Na Ambata Wasu Sunnoni Da Muke koyon Dab'u Na kawarai a kansu

Manzon Allah صَلَّى اللّٰه عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم Yace : 'Wanda Duk Yake Son Sunnah-ta Wannan Yana Sona Wanda Kuma Yake Sona Muna Tare Dashi A Aljannah.' *(Ibn 'Asākir, Mujallad. 9,shafi. 343)*

## 15 Sunnoni Da Wasu Halaye Yayin Tafiya Da Kafa

1. Allah عَزَّوَجَلَّ Yace A Sūraĥ Banī Isrāīl, part 15, verse 37:

وَلَا تَمْشِ فِي الْاَرْضِ مَرَحًا ۚ

إِنَّكَ لَنْ تَخْرِقَ الْاَرْضَ وَ لَنْ تَبْلُغَ الْجِبَالَ طُوْلًا ﴿۳۷﴾

*Kada Kuma Kayi Tafiya A Bayan Kasa Kana Mai Girman Kai , Lallai Kai Bazaka Tsaga Kasa ba {Domin Dagawa} Kuma Baka Kai Tsawon Duwatsu ba .*

*[Kanz-ul-Īmān (Translation of Quran)] (Part 15, Banī Isrāīl, verse 37)*

2. Yazo a Shafi na 78 of *Baĥār-e-Sharī'at*, sashi – the 312-page book – A bugun Maktaba-tul-Madīnaĥ, Sashen Wallafa da Dab'i na Dawat-e-Islami: Manzon Allah صَلَّى اللهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم Yace, 'Mai Daura Kwarjalle Guda 2 Don Takama [Tafiya da Dagawa]. Za'a Danna shi Cikin Kasa Kuma Zaici Gaba Da Tafiya a Kasa Har Ranar Kiyama. *(Ṣaḥīḥ Muslim, Shafi 1156, Ḥadīš̤i 2088)*

3. Manzon Allah صَلَّى اللهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم A Wasu Lokuta Yakan Kama Hannun Sahabin dayake tafiya da Hannayensa Masu Albarka Idan suna Tafiya. *(Al-Mu'jam-ul-Kabīr, mujallad. 7, shafi. 277)*

4. A Duk Lokacin da Yake tafiya صَلَّى اللهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم Yana Dan Sunkuyawa Gaba Kadan Idan ka Kalleshi Sai Kaga kamar yana Gangarowane Daga Tudu صَلَّى اللهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم.

   *(Shamāil-ut-Tirmiżī, Shafi. 87, Ḥadīš̤i 118)*

5. Kda Kajyi Tafiya Da Takama, Saka Sarkar Gwal Koma Dai Takuwane Karfe, Da Bude Gaban Riga Da Bude



www.dawateislami.net

Maballin Riga dan Dagawa {Cewa yasa Sarka} Wannan Shiga Ḥarām ce Ta Irin Mutanen nan ce masu Dagawa. Saboda Haramunne Namiji yasa Sarka.

6. Idan Babu Matsi, Kayi Tafiya a Gefen Hanya Cikin Natsuwa. Bada Sauri-Sauri ba Kana Kutsawa ta cikin mutane Dan Kar ka janyo mutane suna kallonka da Zargi. Kada ka dinga rike Hannun Mutane ko wajan Gaisawa kokuma Runguma datake tattare da Sha'awa .hakan Haramun ne kuma zai kai maiyi sa Wuta.

7. Baya daga Sunnaĥ Kalle-Kalle irin (Wanda Babu Bukatarsa) A yayin Tafiya. Kayi Tafiya Acikin Nutsuwa da Tawali'u Kuma ka Rintse Ganinka. Sayyidi Ḥassān Bin Abī Sinān عَلَيْهِ رَحْمَةُ اللّٰهِ الْحَنَّان Ya Fita Ṣallar Eidi. Lokacin Daya dawo Gida رَحْمَةُ اللّٰهِ عَلَيْه Sai, Matarsa Ta Tambayeshi : Mata Guda Nawa Kagani A Hanya ? Sai رَحْمَةُ اللّٰهِ عَلَيْه Yayi Shiru. Da Matar Ta Dage da Tambaya رَحْمَةُ اللّٰهِ عَلَيْه sai Yace 'Tunda Nafita Idanuna Suna Kallon 'yan yatsuna na {Na Kafa} Har Nadawo.'

*(Kitāb-ul-Wara' ma' Mawsū'aĥ Imām Ibn Abid Dunyā, Mujallad. 1, Shafi. 205)*

سُبْحٰنَ اللّٰه عَزَّوَجَلَّ! Waliyyai Na Kusa da Allah Basa Kallon Nan Su Kalli Chan a Lokacin Tafiya, Musanman idan suna cikin Taron Mutane ko Domin Kada Idanunsu Ya Kalli Abunda Allh ya Haramta Kallonsa walking, a Sharī'aĥ Kunji Yanda Waliyyanmu Suke da Kaskantar Dakai رَحِمَهُمُ اللّٰه.

Hukumcin Wanda Ya Kalli Wata mata Bada Niyyaba kuma Yana Kallon sai Ya Kawar Da kansa Shine Bashida Zunubi.

8. Bai Hallata ba Lekawa Mutane Tagoginsu {Windows} ko kuma Falo Ko Tsakar Gida Batareda da Daliliba.

9. Lokacin da Kake Hawa ko Saukowa daga Matattakala Ta Bene Ka Tabbata Cewa Takalmanka basa Kara Saboda Manzon mu Manzon Rahma. صَلَّى اللهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم Byason Karar Da Take Fitowa daga Takalma .

10. Idan Mata Guda Biyu na Tafiya a Gabanka kada Rabasu biyu Yayin wucewa Hakan Haramunne Kamar Yadda Hanin haka yazo a Hadisi.

11. Tofar da miyau, Kwakwular Hanci, Saka danyatsa a Hanci, Ayi ta faman Sosa Kunne, Cire Kazanta Daga Jiki da Hannaye, Ayi ta Faman Sosa Alaura etc. A gaban mutane ko a yayin tafiya duk bai daceba baiyi kama da halin Nagartaba.

12. Wasu Mutane Suna da Halin Yin ball da Duka bin da shiaga Gabansu, Wannan ba Haline na Wadanda suka waye ba Hakan ma kuma zai iya ji musu ciwo a kafa. Yin ball da Robar Ruwa, Kwali, Kwalba, da sauransu ba Dabi'a ce ta Rashin Da'a Furthermore,.

13. While walking, abide by the laws that are not contrary to Sharī'aĥ. For example, use the zebra crossings or the

overhead bridges whilst crossing the road, if available.

14. Idan kana Tafiya ka kiyaye duk Dokokin da basuci karo da Shari'a ba Kamar Zanen {Zebra Crossing} Tareda Bin Dukkan Dokokin Hanya. Idan kana a tsakiyar Hanya zaka Tsallaka Titi sai kaga Mota ta Nufoka Maimakon Ka Girka a Guje ka Nutsu Tukunna yin hakan yafi a gareka. Hakakuma ,Wajen Tsallaka Layin dogo ayayin Damuna kokuma ana Ruwa Kada ka Taba Dauka cewa Jirgin yana nesa dakai idan Jirgi ya taho dan tsoron makalewa a Layin Dogo kokuma a jikin Wayoyin lantarki Kukuma Jirgin ya taka ka Allah ya kiyaye. A Wasu wurare ma Sam AKwai dokar Tsallaka layin Dogo Ako ina a kiyaye irin wadannan

15. Kayi Tafiya minti 45 Kadinga Żikiri Da Salatin Annabi صَلَّى اللهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم A kullum Tareda Niyyar samun Karfin Bautawa Allah اِنْ شَآءَاللّٰه عَزَّوَجَلَّ, Zaka Zauna da Lafiya. Kayi Sassarfa 15 Matsakaici kuma minti 15 Sanann Sassarfa kuma minti 15. Idan Kayi Hakan nan Dukkan Jikinka zai Motsa. اِنْ شَآءَاللّٰه عَزَّوَجَلَّ Dukkannin 'Yan hanjinka Zasu samu kuzari اِنْ شَآءَاللّٰه عَزَّوَجَلَّ; Zaka Samu lafiya Kuma karabu da Kanana har Da Manyan Cututtuka

Domin koyar Sunnoni Masu Yawa, Ka Dinga sayen Littafai wanda daga Maktab-tul-Madīnaĥ: (1) *Baĥār-e-Sharī'at*, kashi na Mai kunshe da Shafi 312 da (2) *Sunnatayn aur Ādāb* Mai shafi

120 Wata Kyakyawar hanyar koyan Sunnah Shine Shiga cikin Tawagar masoya Manzon Allah Madanī Qāfilaĥs Ta Dawat-e-Islami.

*Lūṫnay raḥmatayn Qāfilay mayn chalo*
*Sīkĥnay Sunnatayn Qāfilay mayn chalo*
*Ĥaun gī ḥal mushkilayn Qāfilay mayn chalo*
*Khatm ĥaun shāmatayn Qāfilay mayn chalo*

*Domin samun Gafara Madanī Qāfilaĥ*
*Domin koyan Sunnah Madanī Qāfilaĥ*
*Domin Magance Wahala Madanī Qāfilaĥ*
*To Madanī Qāfilaĥ*

صَلُّوْا عَلَى الْحَبِيْب صَلَّى اللهُ عَلٰى مُحَمَّد

## Tsarkake Niyyah Wajen Sauraron Karatu

(Masu Kallon Gidan TVna Madanī Channel Zasu Kudure Wadannan Al'amura Aransu.)

- ❖ Zanyi kasa da Ganina a Lokacin Danake Sauraron karatun.
- ❖ Maimakon Nazauna a Jingine da Bango etc., Zan Zauna na Tankwashe Kafafuna irn zama Sallah Domin Girmama Ilmi.
- ❖ Idan dakwai Dama Zan Matsawa Wani Kusa dani dan Shima ya Samu Wajen Karatu,
- ❖ Haka kuma, Idan Wani ya tureni zanyi HakuriZan Kauda kai daga masu Kallona {domin ganin mai zanyi}Bazayi masa Ihu ba Balle Musu.
- ❖ Idan Naji Ance صَلُّوْا عَلَى الْحَبِيْب, اُذْكُرُوا الله, تُوْبُوْا اِلَى الله etc., Zan Amsa Afili iyakacin iya wata Domin Samun Lada, Da kuma Jin Dadin wanda ya furta Kalamar
- ❖ Bayan daukar karatu, Zamu Gaggaisa da mutane ,wasu kuma inayi musu Sallama

صَلُّوْا عَلَى الْحَبِيْب      صَلَّى اللهُ عَلٰى مُحَمَّد

الحمد لله رب العلمين والصلوة والسلام على سيد المرسلين اما بعد فاعوذ بالله من الشيطن الرجيم بسم الله الرحمن الرحيم

## DOMIN ZAMA MUSULMI MAI NAGARTA MAI RIKO DA SALLAH

Tafiyar da dukkan Daren ka a wajen Taron Ijtima' Na Dawat-e-Islami , Wanda ake Gabatarwa Duk Ranar Alhamis Bayan Sallar  Maghrib a Garinku ,Domin Neman Yardar Allah عزوجل Tareda kulla Niyyar koyon Sunnoni . Mayar dashi  Halinka tafiya cikin tawagar Madani Qafilah kwana 3 a Duk Farkon Watan Musulumci Tareda  Masoya Ma'aiki , Tareda cike Katin Madani In'amaat a kullum domin samun Fikr-e-Madinah Tareda Bayarda shi ga Wanda ya dace daga cikin 'Yan uwa Wanda Alhakin Karba yake Kansa a Garinku kwana Goman  Farkon  Watan Musulumci.

Manufar mu itace: 'Zamuyi kokarin sauya kawunan mu  da mutanen  Duniya  ان شاء الله عزوجل Domin sauya kawunan mu , Sai Muna Amfani da  Katinmu na Madani In'amaat  San Nan kuma Kokarin kawo sauyi ga Mutanen  Duniya  Sai Muna shiga cikin Tawagar Matafiya Madani Qafilahs ان شاء الله عزوجل

MADANI CHANNEL

DAWAT-E-ISLAMI

Aalami Madani Markaz, Faizan-e-Madinah, Mahallah Saudagaran
Purani Sabzi Mandi, Karachi, Pakistan
UAN: +92 21 111 25 26 92 | Ext: 7213
Web: www.maktabatulmadinah.com | E-mail: feedback@maktabatulmadinah.com